UNHCR
L'Agence des Nations Unies pour les réfugiés

FICHE PRATIQUE

# MAFI KARANCIN KA'IDOJI AKAN KORAFE-KORAFE DA RA'AYOYI

MUTANE NADA HAKKIN YIN KORAFI DA BADA RA'AYIN SU ZUWA WANI MAI GUDANAR DA SHIRYE-SHIRYE DA KUMA SAMUN AMSAR DA TA DACE AKAN LOKACI. WANNAN JERIN ABUBUWA NADA MANUFAR TALLAFAWA KUNGIYOYI DA TANTANCE KO SUN CIKA MAFI KARANCIN KA'IDODI NA SAMUN TSARURRUKAN KARƁAR KORAFE-KORAFE DA RA'AYOYI.

## MENENE TSARIN KARƁAR KORAFE-KORAFE, RA'AYOYI DA BADA AMSA ?

Tsarin karɓar korafe-korafe, ra'ayoyi da bada amsa (CFRM)* shine wani jerin hanyoyi a bayyane, wanda ke bawa mutane a cikin al'ummomi damar wani hanya mai aminci, sirri na bayyana korafe-korafen su ko bada ra'ayoyin su akan abubuwan da suka fuskanta tare da hidimomin da suke amfani dasu.

Asalin manufar shine don ƙara tasirin al'ummomi akan hidimomi, tabbatar cewa an magance matsalolin rashin gamsuwa da wani hidima ko rashin da'a daga ma'aikata, kuma don ƙarfafa ingancin shirin gabadaya da tabbatar da dorewar tsarin.

## MATAKAI DON KAFA WANI TSARIN KARƁAR KORAFE-KORAFE DA RA'AYOYI

### 1. SHIRYA

- Samu alƙawarin ƙungiya don ƙafa wani tsarin karɓar korafe-korafe, ra'ayoyi da bada amsa wanda ya dace da rukunai jama'a da ake nufa
- Tattauna da al'ummomi da ɗai-ɗaikun mutane daga rukunai jama'a daban-daban (maza, mata, yan mata da yara maza, tsofaffin mutane, mutane masu nakasa da sauransu) akan buƙatun su, abubuwan da suka fi so, da samuwa (musamman a lokacin tallafi daga nesa, wannan yana la'akari da samuwar intanet)
- Bayyana dalili, abubuwan da ya ƙunsa da abubuwan da ake tsammani.
  - Tattaunawa tare da al'ummomi: Ya kamata a tattauna tare da al'ummomi a matakin tsara tsarin don tabbatar tsarin yana samuwa, akwai aminci da daranjantawa da kuma gujin jawo illa. Yana da mahimmanci a bada dama ga wanda suka fi cikin rauni don bari su samu damar wuraren shiga da samun bayani, wannan yana nufin tattaunawa da mutane masu nakasa, tsofaffi, gidajen da mata ke shugabanta, mata da yaran da suke cikin haɗari da sauransu. Sannan ya kamata a riƙa tattauna da al'ummar a kowace shekara don tantance da kimanta CFRM.

**FICHE PRATIQUE**

- ◦ Lura da abubuwan da ake tsammani: Wannan yana da mahimmanci, saboda al'ummomi zasu iya ganin cewa tsarin karɓar korafe-korafe da ra'ayoyi na iya magance dukkan matsalolin su. Kuma tsara waɗansu korafe-korafe za'a iya bada amsa kuma wannene ba za'a iya ba, amma kuma zasu taimaka wajen yanke shawarwari game da shirye-shirye da tallafi.

## TSARAWA



- Gano waɗansu hanyoyin sadarwa suka fi dacewa
- Yi la'akari da yadda sirrin bayanin yake kamar yadda za'a karɓa bayanin PSEA da magance shi
- Zaɓa rawar da kowa zai taka, ƙafa kayan aiki kuma ya kamata ma'aikata su samu horo akan sadarwa da mutanen da rikici ya shafa/masu rauni, da kuma yadda za'a amfani da tsarin da kuma su san yadda za'a tsara hidimomi - don tabbatar sun bawa masu cin gajiyar bayanai da suke buƙata idan an tambaya
- Jawo hankalin al'umma akan yadda ake tsammani za'a amfani dashi, dalilin tsarin da yadda za'ayi korafi
- Ma'aikatan da aka zaɓa na gudanar da korafe-korafe ya kamata su zama daban da masu aiwatar da shirye-shirye, da kowane irin aiki a cikin ƙungiyar wanda zai haɗa su da masu cin gajiyar da kayyayaki. Banda ma'aikatan M&E kawai kuma wannan ya danganta akan wanda mai aikin ya ke bada rahoto zuwa.

### Hanyoyin Sadarwa:

Yi la'akari a hankali, tare da tattauna da al'umma, amfani da rashin amfanin kowace hanyar sadarwa kafin a zaɓa - layin kar ta kwana na bayani, akwatin korafe-korafe, email, Facebook, WhatsApp, a zahiri. Ya kamata dukkan gungun su samu damar mahadi akan bayanin hanyoyi daban-daban.



### Bayanan da zasu iya bada matsala:

Bayanai sirri (masu alaƙa da rashawa, amfani da dama da cin zarafi ta fuskar jima'i, ko babban rashin da'a ko rashin bin dokokin aiki) da bayanai da ba sirri (misali ƙaluɓale wajen amfani da sharudda zaɓa) zai yiwu a tattara. Bayanai sirri da aka samu na buƙatar bada amsa da gaggawa ga wani mai bada hidimar na musamman. Ya kamata ma'aikatan da suke karɓar korafe-korafe da ra'ayoyi su samu horo akan yadda zasu bada amsa ga bayanai sirri da ka'idodin turawa gaba da shaida masu aminci. Ana ƙarfafa a samu ma'aikata maza da mata kuma daga wurare daban-daban don taimakawa wajen bada amsa skan lokaci kuma ta hanyar aminci da sirri

FICHE PRATIQUE

## TATTARA BAYANAI, NAZARI DA RABAWA



- Shirya yadda za'a samu, adana da tabbatar da wani korafi ko ra'ayi da aka samu yayin girmamawa sirri , da ka'idodin “kada a cutar”
- Shirya tattara bayani wanda ma'aikata suke buƙata da gaskiye don yanke shawarwari kuma sauya shirye-shirye (misali samar da rahoto, bada shawarwari)
- Tabbatar an ɗauki kuma anyi nazari akan ra'ayoyin da aka nema da wanda ba'a nema ba
- Shirya wanene zai yi nazari akan bayanin kuma wanene zai karɓa
- Bada rahoto akan yanayin ra'ayoyin da ake samu da sakamakon nazari akai ga masu yanke shawarwari
- Ya kamata a haɗa kuma a aiwatar da ka'idodin kare bayanai a dukkan matakai CFRM (Tsarin Karɓar Korafe-korafe, Ra'ayoyi da Bada amsa na Al'umma). Yana da mahimmanci lura da sirrin wanda ya kawo korafin koda s cikin ƙungiyar don gujin fansa da mummunan sakamako ga mai korafin, daga ma'aikata, abokanai aiki da masu kawo kaya.



### Matsayin korafe-korafe da ra'ayoyi:

Ya kamata a sa alamar a buɗe ko an rufe akan korafe-korafe da ra'ayoyi, kuma ya kamata a rubuta kwanan watan da aka rufe korafin ko ra'ayin. Ya kamata ma'aikata su samu horo akan yadda zasu adana korafe-korafe da ra'ayoyi, don tabbatar an raba su da adana su daidai tsakanin ma'aikatan.

### Magance korafe-korafe da ra'ayoyi:

Bayan an samu kuma an ɗauki bayanin wani korafi ko ra'ayi, ya kamata a tura korafe-korafen zuwa jami'in da suka dace na cikin gida don bincike da bibiya. Sai ma'aikatan da suka samu horo kawai zasu yi bibiya da bincike, idan hakan ba zai yiwu ba ya kamata a yi amfani da tsarurrukan rahoto na ƙasar*. Idan korafin ko ra'ayin bai shafin shirye-shiryen ƙungiyar ku, ya kamata a tura zuwa ƙungiyar da ya dace don a ɗauki mataki tare da neman izini.

## BADA BAYANI KO AMSA

- Kafa hanyoyin magance wani korafi ko amsa zuwa wani ra'ayi (turawa gaba, ba tare da wani tsari, da tsari ko ta bincike)
- Tabbatar akwai tsarin daukaka kara masu aiki kuma a bayyane, kuma an sanar da al'umma
- Inda zai yiwu ya kamata ƙungiyar su tantance matakin gamsuwa da amsar da matakin da aka ɗauka kafin rufe shi



Plus d'outils
et de conseils
pour communiquer avec les communautés sur le site :
cwc.westafrica.exposed